#Hattara mata! hattara!! Ina matan nan daga Aure ku sakar wa miji jiki , yayi ta sukuwa yana wangale ku ,ke adole miji daɗi sex daɗi to hattara wallahi idan ya jirkita ki ,ke naki sai yafi nasu Dudu muni ,don su da ƙuruciya sunci tuwon dawa,ke me kika ci? Indomie talia,kayan maƙulashe kawai ,kuma har kike tunanin kiyi ƙwari da lafiya .bayan kin bar kanki yana ta sukuwa yagama gwagwgwale ki kina miji So ! Sorry for you Hjy Zaki ga yanda zaki koma gaba.

#Wasu ma har so suke ayi sex dasu a rana sau uku sau huɗu biyar ,wai so ne! Wata kuma supliment na ni'ima ta shasu roba roba tayi matsi dana Matsawa a gaban ta...wurin yayi raga raga gaba wallahi mu kiyaye ...wai a wannan zamanin har shi da kanshi namijin ke tausaya mawa durin yana tunanin gaba anya zaiyi ƙarko? Hummmm mu kiyaye komai ayi saffa saffa don Allah.

❀❀✿

Zaune suke su kusan biyar a titi a wulaƙance a ya ƙune fata a tattare na wahala sai tsantsan shahara a zuciyar su. Miƙewa Balaraba tayi tana gyara yafen ta cikin harshen Hausa take faɗin bari na samo rushi wurin mai shayi.... Ke Balaraba mai zakiyi da Rushi da wannan sanyin safiyar? Cewan Rabi tana kallon Balaraba tare da mata kallon tuhuma...aikin san me xanyi dashi sarai ko gulma ne?. Tayi maganan tana wucewa fuuuu tare da Nufar mai shayi dake can tsallakersu... Allah sarki bayin Allah. Abun da Rabi tace kenan don tare suke da Balaraba ,sai dai ita sadaka yalla take da bararar ta ,akasin Balaraba dake maita a sakaye babu wanda ya sani sai su yasu yasu yɤan uwan ta...tana sadaka yalla daga haka kai namiji kaga sadaka yalla ko tace karuwa kace muje ,kunyi masha'anku ka ƙwaƙuleta kayi release kaji daɗi ...to ka sani daga lokacin da kuka rabu kayi ban ƙwana da duk wani jin daɗi sai ta kaika rabari ,don da yawa Mayu ne sai ɗai ɗai....a haka taci mutane ta kashe har lahira babu iyaka yanxu ma ta tafi samo rushi ne da zatayi gashin kurwa ta lasa har tacinye duk.....

Free page bafa zaiyi yawa ba ga masu buƙata zasu iya fara biya tun yanxu...Littafin na kuɗi ne Regular payment₦300 VIP membership ₦600 Spc 1k...Zaki iya turo da kuɗin ki ta wannan asusun bank account 6037312299 Mohammed A'isha Keystone bank ko ki tura katin MTN ta wannan Numbobi nawa 08081202932 ɣan Niger zaku biya 600f katin airtel...

#Shere pls

ANTY AISHA MMN TEDDY

[11/4, 11:41 AM] ANTY AISHA MMN TEDDY: *SADAKA YALLA!*

(Baraa ko karuwanci! Funny, romantic and sympathy story)♀

Free page

005

AUNTY AISHA MMN TEDDY

Free page zai ƙare nan kusa Littafin na kuɗi ne Regular payment₦300 VIP membership ₦600 Spc 1k...Zaki iya turo da kuɗin ki ta wannan asusun bank account 6037312299 Mohammed A'isha Keystone bank ko ki tura katin MTN ta wannan Numbobi nawa 08081202932 yʻan Niger zaku biya 600f katin airtel... VTU trnsfer sai ku tura ta wannan number 09061466409

❁❁✿✿

Masu buƙatar duk ka littafaina zasu na same su complete Inshaallh

Walijaam₦300

Siyasata₦300

Gidan ƙwarata₦200

Yʻar Aiki na₦100

Dijama yʻar Fulani ₦200

My lady boss₦500

Yʻar maula ₦300

Kʻwarton manya #500

Bintoto

Taɓara₦500

Kawaliya₦300

Zuma da maɗaci₦200

Kʻwaryar sama₦300

Gidan zawarawa₦300

Habibi da'iman da dai sauran su;

Suna nan zaune Balaraba ta nufi wurin mai shayin ,wanda abunka ga wasu Hausawan mu yʻan iska ,sun bar na gida da kuka amma sun taho wurin mai shayi ana masu shayi susha kakkaura sun bar mata a gida da fatsamin yʻayʻa. Duk

wannan ma bai ishe su ba ,sai sun bi Sadaka yalla na titi ,wanda basa da farashi ko kaɗan . Kabar dai dai ka koma ma haramun wanda zaka ci wutan Ubangiji. Tun isowar balaraba idon Rabo mijin Hausi ya sauka akan ta ,sai wani shafa talliyar sa yake yi ,don irin mazan nan ne masu aske suman kan su sol² . A balarabiya kece? ...fuska babu yabo ba fallasa don ba hausan take ganewa sosai ba tace " Eae. Bakin shi ya yashe fatsamin haƙoran sa da suka yo gantso gaba kuma a ware suka bayyana gasu a ware abun ba sha'awa duka suka bayyana. Cewa yake" Ai ku kyaun bashi da banbanci dana larabawa kin ga ai yayi dai dai dana ce balarabiya....kuji jahilci! Murmushi Balaraba tayi tana bin timbinsa da kallo da yayi gaba rimmm... Tana kallon yanda mansa da ɓargon sa ke zagaye jini...tuni ta fara tanɗar harshe tana add'ua a zuciyar ta Allah yasa Rabo ya taya...Balaraba yanxu sai ina? Gashi ina Son mu keɓe. Murmushi Tayi tana ware idanun ta akan sa wanda gashin ido sukayi masu rumfa. Gaushi nazo samu anan ,amma bari na samu yanzu zan taho....to ina bukatar ki balaraba ... murmushi Balaraba tayi tana bamawa mai shayi ƙwanon yana zuwa ba mata gaushin . Jiki na rawa ta koma can gyefen bakin hanyar da suke zama...bayan wani langye² ta nufa ,tana fara sana'ar soya kurwan mazan da ta kama ,masu neman mata tun kana yi da yɑn tasha ka ƙare mawa Sadaka yalla har a haɗu da mayya.

❁❁✿✿

Ɓangaren Abdul Ahaad kuwa manyan ƙasan Nigeria ne sukayi ɗauki hayar su zuwa cikin garuruwa da inda duk wasu muyagu suka addabi al'umma sai da aka yi rubutun shi tamkar map sai da aka zana komai a inda zasu nufa harda wannan dajin Kidandan . Masu kidnpers kam da sauran yɑn fashi tun da suka ji labarin abun da shuwagabannin Nigeria sukayi na ɗauko sojojin haya akan yaƙar su ,kuma wasu sun su da yawa sun san su waye Su Abdul Ahaad ,don su sun fi ƙarfin Soja ,sune sojojin nan masu jan hula , wanda ake kira da sojan Sojoji ,idan soja yayi ido biyu dasu gudu suke inkuwa sojojin mu sun kai ɗari zaka ga suna darewa . Basa yarda suyi ido biyu dasu . Su dama irin wa'anan army police ba'a fito da irin su sai irin ƙasa na cikin matsanancin tashin hankali ,don su ba'a ganin su sai a irin wannan lokaci ko idan anci ƙasa da yaƙi shine ake sakin su kaman damusa. A lokacin da aka ji labarin guduwar Abdul Ahaad da abokan nan biyu Nigeria tsorata tayi , don manya da gudu sun bar Nigeria a cewan su ba za'a ƙara shekara ba Nigeria za wayi gari babu kowa ,tun da har sojan Sojoji ya gudu saboda fitinan boko haram. Jin yanzu sun dawo korar kidnpers don sunfi ƙarfin suyi yaki dasu ..idan sukace yaƙi zasuyi dasu to tabbas bazasuyi sati ba zasu fatattaki duk wani ɓarayin Fulani da kuma ɓarayin mutane na nan gida Nigeria... alhmdllh kuma tun da kidnpers sukaji labarin saukar army police sunji ance an watsa su a daji ,wannan yasa su fara hijira suna guduwa daga duk wani dajin da suke...don sun san army police Idan suka ka maka kisa basu ɗauke shi a bakin komai ba. Abun kuma da ya basu tsoro na biyu shine , rantsuwa da sukayi na ganin bayan duk wasu yɑn ta'adda , za kuma su tsaya koda zasu rasa rayukan su. Kuɗaɗe ne shugabannin Nigeria suka ba ko wannensu billions ,Wanda

zasu bar ma iyalan su ,don shi soja irin wa'anan Basu san zafin kudi ba ,komai nasu na matan sune da iyaye. Haka kowa yayi sallama da iyayen shi da yan uwa cike da kewar zasu dawo wata Allah kuma basu dawo ba ! .

❁❁✿✿

RUGAR KIDANDAN!

Kallon Baaban nata Shatu keyi ,tare da sauraren ta ,tana sa hannu tare da amsar ƙwaryar da babu komai cikin ta ...kiyi sauri kisamo masu ganyen sarke , insun sha Zasu samu sauƙin zogin raunukan jikin su ". Baaba ke maganan yayin da Shatu ke faɗin to Baaba . Juyawa tayi tana barin bukkan nasu , wanda idan ka fito fili zaka gani tata dajin Allah babu kowa sai tsirarun bukkan fulanin... Tafiya take mai nisan zango ,wanda tun tana hango bukkan su da tsirarun fulanin har ta daina a haka ta nitsa cikin daji kan ta tsaye babu tsoro don sun riga sun saba da wannan rayuwar. Haka take tsalleke mugayen dabbobi a hankali tana ƙara nitsa cikin dajin. Wani zanzaro tazo mai duhun gaske , bishiyoyi ƙasa ƙasa sunyi rumfa sun ƙare rana ,sam baya hasko wurin , kaman ba rana ba ....yanda kasan dare haka wannan wuri yake. Cike da jarumta irin nata mace mai kamar maza yarinya yar shekara sha shida takai hannun ta tana buɗe hanya tana kutsawa ta cikin bishiyoyin da macizai ganin ba komai bane a wurin.

Wata bishiya takai hannun ta ,tana tsinkar ganyen ta tare da zubawa cikin ƙwaryar nata , sai da ta ɗan ɗiba da yawa ,kamin tayi gaba zuwa wani bishiyar....hayaƙi ne taga yayo inda take...da hasken zafin ciyayi ...alamu da mutane a kusa da ita. Duƙawa tayi tana ɗaukar ƙwaryar ta babu tsoro tare da ɗaukar wani sanda ta irin bugayen fulanin nan ,wanda suna buga maka ita sai gawa don ko shurawa ba xakayi ba ....

❁❁✿✿

Sosai suke mamakin ganin mutum a irin wannan daji ,Bama wai namiji ba ,mace ...tun da ta yanko wannan baƙin dajin tana tsinkar ganyen ta , duk suna kallon ta ...suna zaune sun kama wata dabba dana kasa gane meye ? Sun banƙare ta suna gasa namar ta kowa na yanka. Yana ci ...yanda suke zaune sun maida wurin ɗakin uwar su ,ba kace wai sun san wata rayuwa jindaɗi ba...dukan su yayan gata ne gaba da baya ,Son sojan ajinin su take .... babu wanda ya motsa sai Nura ne ya kalli Abdul Ahaad yana cewa" Ahaad kaga mace mai kaman kai kuwa? . Kallon ban gane ba ya watsa masa ,yana cigaba da zugar sigarin sa . Murmushi Nura yayi yana cewa " Jarumtar mana ,mace da Jarumtar shigowa wannan baƙin dajin ai itama a mata jagaba ce! .wani irin murmushi Abdul yayi wanda tun shigowan su dajin baiyi

ba...kamin ya miƙe yana cewa to bari mu gani anya jaruman ce?. Yana faɗin haka ya tashi cikin takonsa ,wanda shi idan yana tafiya baka jin takon sa ...sai dai ƙamshin sa.

Itako Shatu Sandar ta ta ɗauka tana jirar da wa Allah zai haɗa ta? Ta buga masa ko mai ya same shi bata damu ba...a tunanin ta ɓarayin ne kaman yanda suka saba damunsu...sudai ƙwana biyu sun ji shiru babu ɓarayin da masu satar mutane ,basu san dalili ba ,don basu san gomnati ta kawo masu sojojin Haya ba...Army police. Motsi taji a bayan ta ,wanda yasata saurin juyowa ,wayam babu kowa..... Tsayawa tayi tana tunanin ko dabbobi n dajin ne ....sai taji an ja mata gashin kan ta da yake a tufke , nan take ya barbazu har gadon bayan ta. Sandar ta ta ɗaga tana juyowa a zafafe tare da ƙwaɗota ga ko waye...kawai sai taji caraffff an riƙe Sandar..... Wani irin kallo take masa , tare da bin gaɓɓan sa da ido zufa ne ya fara tsiyayar mata na tsoro ...bata taɓa ganin mutum irin wannan ba.idanun sa ya watsa mata da suke lulu a warwaje daƙwa² . Ta koma can ƙasan sa ....ko kafaɗan sa bata kai ba ,duk da take doguwa. Faffaɗan ƙirjin sa ta kalla tsoro ne ya dirar mata ,a zuciyar ta tana tamtaman mutum ko aljan?

#SHARE

[11/6, 8:21 AM] ANTY AISHA MMN TEDDY: *SADAKA YALLA!*

(Baraa ko karuwanci! Funny, romantic and sympathy story)

006

❁❁✿✿

Masu buƙatar duk ka littafaina zasu na same su complete Inshaallh

Walijaam₦300

Siyasata₦300

Gidan ƙwarata₦200

Yʻar Aiki na₦100

Dijama yʻar Fulani ₦200

My lady boss₦500

Yʻar maula ₦300

Kʻwarton manya #500

Bintoto

Taɓara₦500

Kawaliya₦300

Zuma da madʻaci₦200

Kʻwaryar sama₦300

Gidan zawarawa₦300

Habibi da'iman da dai sauran su;

❁❁✿✿

Jikin Shatu fulfulbe ne yayi sanyi na tsoro , tsayawa tayi ƙurr tana kallon sa kamin a hankali ta sauke Sandar ta ƙasa ...Shi kuwa ganin tsoro a idanun ta yasa shi ɗan sassauta fuska , kallon tuhuma da rashin fahimta take masa wannan yasa shi kai tsaye miƙa hannun shi yana sawa cikin rigar shi ,don ba shigar soja a tare dashi , normal shiga ce ta ƙanun kaya , wannan yasa Shatu gaza fahimtar haƙiƙanin shi ɗin waye? Kuma take masa kallon ko yana ɗaya daga cikin ɓarayin shanun su ...don haka suke kirar kidnpers. Fiddo mata yayi da ID card nashi na soja , wanda taga bugun hoton shi da kayan sojoji . Babu magana tasa kan ta tana shirin juyawa shi miskilanci ita kuma duk da gwana ce ta surutu shiru ta masa don har a lokacin tsoron bai gama sakin ta ba...Ganin ta duƙa ta ɗauki Sandar ta tana shirin tafiya yasa shi shan gaban ta yana cewa " Ke me kikeyi a wannan dajin mai haɗari a wannan lokaci?. Kallon sa tayi tana sakar masa murmushi kamin tace " Sunana Shatu! Kaga rugar mu can, magani na taho samun ma wazon da sauran fulanin mu. Tun da ta fara maganan yaji jin sa da ganin sa ya ɗauke , sakamakon jin sanyayyar kuma zaƙaƙƙar Muryar ta....lumshe lulun idanun sa yayi a hankali yana fara tuno da ganin ta na farko da ya taɓa yi a rayuwa a tashar watsa labarai na Najeriya.

Bari nayi sauri Baaban fulfulbe na jurar na! Yaji Muryar ta a karo na biyu ya katse sa , nisawa yayi yana cewa " Ok muje nayi maki rakiya! Kallon sa tayi tana faɗin " Rugar mu? . Gyaɗa mata kai yayi yana gaba ,kaman wanda yasan hanya ...shidai kawai zuciyar sa takasa amintar yana gani ya bar mace ta ƙara nutsa cikin dajin ita

kaɗai ,wannan yasa shi yanke shawarar ya mayar da ita rugar tasu. Murmushi Shatu tayi tana bin bayan sa ,wanda su Nura ke cewa " To wancen ina zashi kuma haka??? Cike da shakiyanci Samir yace " yaga yɾar Fulani kyakykyawa fulfulbe ta fi da zuciyar Abdul Ahaad. Dariya Nura yayi yana faɗin ina kai wannan ƙarya ne, da aƙwai dai dalilin sa nayin hakan.

A gaɓar wata ruwa yaga Shatu ta tsaya , tana zama gyefen Ruwan , don ita sam ta manta da mutum wai suke tare , kasancewar ta saba shigowa ita ɗaya , kuma shi da suke tafe bai ce mata uhmm .uhm'uhm ba. Zama tayi tana sa hannun ta cikin ruwa n tare da saka ƙafafun ta duk , a ciki tana wasa da ruwan tare da dariya tana waƙoƙin ta na Fulani. Can gyefe yajah ya tsaya a wannan fatsatsin Ranan da rabon da yaji irin ta ya manta . Tun ana ƙwararar mintuna ya koma a wanni , fahimtar wacece Shatu ,don ya fahimci ita yarinya ce mai shegen wasa ,idan ya barta zata kai yammaci wannan yasa shi takawa zuwa inda take ". Kee ". Taji ya Kira sunan ta , cikin sauri ta juyo tana kallon sa sam ta manta da wai wani bil'adam suna tare. Nace maka Sunana Shatu . Tayo maganan tana ɗan turo bakin ta gaba na tsiwa ,ba ta jira jin mai zaice ba ,ta cigaba da cewa " Na tafi Ruga ko? Don tasan shine abun da zaice mata. Gyaɗa kan sa yayi yana lumshe idanun sa tare da buɗesu Alamun eh".

Miƙewa tayi da sauri tana ɗaukar ƙwaryar tare da ɗauka ta bisa tsakar kan ta tana cike da ƙiriniya ta ƙuruciya na yaran nan masu gir'gir tace " Wanxan gani nan zuwa! Tayi maganan tana shirin barin wurin ,sai kuma ta juyo tana cewa" Hamma! Kallon me kika ce yayi mata, don baiji kuma bai fahimtar mai tace masa ba". Murmushi tayi tana cigaba da cewa " Hamma kana ɗan binni mai ya kawo ka dajin ƙauyen Fulani? Mu fa Fulani ne na ƙauye! Ko baka gani ba. Murmushi yayi mata yana kai hannun sa tare da ɗaukar Sandar ta da ta manta dashi gyefe yana motsa laɓɓan sa da cewa " Ni Soja ne ,zana iya rayuwa a inda yafi nan zama daji ba abun mmki bane ba. Maza tafi ki kai masu maganin su. Yayi maganan yana kai hannun sa tare da dafa kafaɗan ta alamun su tafi. Saurin Matsawa Shatu tayi tana kallon sa kamin tace " Kai nifa matar Aure ce! Dammmmmm yaji ƙirjin shi ta buga...manyan idanun sa ya watsa mata yana bin ta da kallon she's mad ,Banda hauka nawa take da zata ce masa ita matar Aure ce. Zuciyar sa ce ta basa amsa da faɗin " Dama idan surutu yayi yawa ƙarya na shigowa ciki, kalla yanayin ta ta cika zuba kaman gidan Radio'n BBC . Ok sorry ! Yayi maganan yana ɗan Matsawa gyefen ta . Me kace? Ta katse shi don itama batasan meye wani Sorry ba! Maganan ta ta fara masa yawa ,wannan yasa shi cewa " Muje ko". To ta basa amsa tana yin gaba....a haka suka dinga wuce ƙoramao iri iri masu ban tsoro da dajuka , bai bar Shatu ba sai da ya hango bukkan su na Fulani yana fara hango tsorarun fulanin sannan ya juya ba tare da yace mata komai ba. Ita ko Shatu da bata san ya tafi ba , har ta fara isowa gab da bukkan su ne ta buɗe baki cikin zazzaƙar Muryar ta tana ƙwado kirar Baaban fulfulbe na dawo!

Sai kuma ta cigaba da cewa " Kaga Hamma nan ne bukkan mu , ga bukka n baaba ta ,gana jauro ,wancen na wanzan..... shatu kedawa kike zuba surutu ke kaɗai? Baaba ta fito tana duban Shatu cike da mmkin Shatu ta juya tana cewa " Kai Baaba ina yake?.

Wake nan ? Baaba tayi maganan tana kallon gyefen da Shatu ke kallo. Baaba dashi Fah muka taho wurinan! Shatu Anya baki ƙwaso miyagu ba a dajin nan da kika shiga da rana? Waye zaki gani a daji a yanxu ,musamman yanda rayuwa ta kasance?. Murmushi Shatu tayi tana cewa " A'a Baaba shine yanxu Fah muke tare dashi...dogo fari yana da suma ƙwantattu irin....Wanzo? Wanzo?? Baaban fulfulbe ta fara kirar sunayen mutanen fulanin kowa yazo bakin ta...Kamin kace kobo tuni mata da mazan da sukayi saura sun fito suna faɗin Inna an Wara Yadikko". Wanzan ne ya fito yana ɗingisa ƙafa da yasha dukan barayin sun masa karaya kusan uku a ƙafa ɗaya. Gwagwgwo meke faruwa? .

Ku kira liman Shatu ta fara hauka , miyagu sun shafe ta. Da jin haka basu tsaya tambayar me ya faru ba ...suka banzama niman Liman don sun san Baaban fulfulbe ba zata faɗi Abun da ba haka ba...yaewindo ne tace " Dama tuni na ke wasuwasun Shatu na da miyagu ,musamman yawon son Rawar ta da shiga dajin ta abun yayi yawa.... Kallon su Shatu keyi kurum sai ta sheƙe da dariya tana nufar bukkan su , tare da shigewa .... yafindo ne tace ma wa Baaban fulfulbe su tsaya a bakin bukkan kar su bari ta fito suyi na daji da ita...jin ko haka mata kusan su huɗu suka tsaya a bakin bukkan wai kar Shatu ta fito ,suna zaman jirar isowan Liman.

❁❁✿✿

Malam Rabi'u ne sai can hantsi ya fito daga ɗakin sa yabar Binta ƙwance ko motsi takasa yi saboda jigata da wahala ...koda ya fito har a lokacin gidan cike yake , Haushi ne ya kama Suwai zuyawa tayi tana basu wuri tana jin malam Rabi'u na tambayar wai meke faruwa? Ana kora masa bayani akan yayi wa ɗan uwan sa me Unguwa ya dawo da matar sa da yasaki yana maganan Sadaka yalla zai Aura yar shekara Shatakwas dai dai shi yana haura shekara saba'in a duniya. To meye aibu a ciki? Abun da malam Rabi'u ya fara cewa kenan! Kamin ya cigaba da cewa" Dama zama zaiyi ba matar shine aibu, kuma naga uku ya riga yayi , ai shikenan sai haƙuri... inalallahi wai'ina ilaihir rajiun...kai tirrrr da wannan gida da mutan cikin ta,

Suwai tayi maganan tana cigaba da tsiyayar da hawaye. Juyawa malam Rabi'u yayi ganin yaran kowa yayi caaa kan abin da yace...don yara ne suke dashi fatsami guda...amma a haka basu san sun girma ba. Tun da suka bar gidan , matan gidan ke cikin tashin hankali , saki da tsufa ,ai ya bari tayi masa takaba tun da saura kwana nawa ne yayi ƙaura sittuna au saba'una to shi yakai har ya wuce. Amma a haka yake da budurwar zuci na son Auren Yar shekara sha taƙwas.

❁❁✿✿

Bedroom ɗin shiru kakeji babu komai dake tashi sai sautin kukan ta ƙasa ƙasa , hasken Dumb light yasani fahimtar Hajiya Ainu wanda gyefe guda Alh Amin Yero ne zaune a ƙayataccen gadon nasa , saman cinyar sa ɗauke da laptop Yana operating system ɗin nashi hankalin sa ƙwance. Kaman waƙe take ba kuka ba ,duk a ƙarƙashin zuciyar sa kuwa yana jin zafin kukan nata. Cikin dasasheshiyar Muryar ta na wanda tayi kuka har ta galabaita ta fara faɗin" Yanxu Alhaji Abun da kakeyi kana kyautawa yayan ka kuwa? Kar ka manta kana cutar dani...Ba ason raina nake zama dakai ba a yanxu ,sai dai ba yanda na iya...Ni ban taɓa zina ba ,Allah ya haɗani da miji m....Aini!! Ya Kira sunan ta yana katse ta...tare da watsa mata idanun sa da suka narke suka tarkade suka ƙyaƙafe suka soye a duniya ....I'm so sorry for that! Nima baa son Raina bane. Dole ne tasa ...kuma yawon maganan yaya da kikeyi nufa ban haihu ba a yanzu yata ɗaya na haifa a rayuwa ,kuma tuni ta daɗe da barin gidan duniya. Baka kuma tunanin Allah ya baka a inda bakayi tunani ba ,idan ta yi aure ta samu miji irin ka , me zaka ce ,kuma me zaka ji...nima Fah yace! Wani irin zafi yaji zuciyar sa na masa akan maganganun matar nasa Hajiya Ainu. Wanda cikin Rufewa r ido ,ba tare da ya tache maganganun bakin sa ba ya fara fitar wa kaman haka; ke yace? Yar wakenan? Kin manta a yanda na Aure ki ba gata! Ni nayi Mako komai na rayuwa! A titi kina Bara na Aure ki a SADAKA YALLA!

#SHARE

Masu buƙatar wannan littafin zasu na iya tuntuɓa na kai tsaye Ta wannan Numbobin 08081202932 / 09061466409 ,if you are not ready ,don Allah Kar Kuyi mun magana I have alot to do! Kar mu ɓata wa juna lokaci...sannan masu tambayar littafaina na kuɗi ne ga farashin ko wanne can a saman page ɗin Sadaka yalla!

[11/6, 6:13 PM] ANTY AISHA MMN TEDDY: *SADAKA YALLA!*

(Baraa ko karuwanci! Funny, romantic and sympathy story)

007

❁❁✿✿

Masu buƙatar duk ka littafaina zasu na same su complete Inshaallh

Walijaam₦300

Siyasata₦300

Gidan ƙwarata₦200

Yʻar Aiki na₦100

Dijama yʻar Fulani ₦200

My lady boss₦500

Yʻar maula ₦300

Kʻwarton manya #500

Bintoto

Taɓara₦500

Kawaliya₦300

Zuma da madʻaci₦200

Kʻwaryar sama₦300

Gidan zawarawa₦300

Habibi da'iman da dai sauran su;

❁❁✿✿

A sadaka yalla na kawo ki a halina , nayi maki Komai na Saki kikayi ilimin addini dana zamani , har a yau kika zama haka mai fadʻa a ji ,kika shahara kika zama

babbar yaɾ siyasa har kike da wannan matsayi na commissioner na sadarwa,ki rinƙa ya isa ! Ta katse shi cike da ɓacin rai tana ɗaga masa hannu alamun dakatarwa. Kƙwarai kayi mun duk wannan abubuwan da jero , kuma na gode! A takaice yanzu gaskiya ce baka so! Shi yasa har ka fara tariyo abubuwa da yawa da suka wuce kake Son faɗa mun a yanxu harda mun gorin ka ganni ina Bara a tsakiyar titi a haka ka Aure Ni ka kawoni a halinka...na gode ƙwarai amma kar ka manta da mutunci na ka Aure Ni ban yasar a titi ba... Maganan Hajiya Ainu ne ya kakere mata sakamakon zuwan wani kuka wanda bata shirya masa ba...kukan ne ya kubɓuce mata ,wanda cike da Muryar kuka ta cigaba da cewa" Na gode mawa Allah da tun kan na mutu na kuma rabu da Zia na sai da na faɗa mata wacece Ni da Asalina. Tun kan tasan meye rayuwar bakin ta da ƙwaƙwalwar ta nasha faɗa mata wannan kalmar na SADAKA YALLA! tasan Mahaifiyar ta ba kowa bace fache mabaraciya! A haka ashe bazamu yi nisan zama ba a rayuwa har mai rabawa ya raba! Nikaina ba'a Son raina na fito yawon sadaka yalla ba ,nabar dangi na nabar ƙasa ta , kai kaico ga matan da suka fara yin wannan sadaka yalla ,har ya zama mana abun koyi yau ga irin ta nan. Jikin Alhaji Aminu Yero ne yayi sanyi ƙalau ,don koba komai yana masifar ƙaunar matar nashi Ainu ,tabbas akan ta da auren su ya fuskanta ƙalubale ,don kowa juya masa baya yayi akan wannan Aure ,wanda har yau mahaifiyar sa Hajiya Didi bata ƙaunar Hajiya Ainu .

Cikin Muryar rarrashi mai tattare da nadama kan abun da ya aikata a yanxu yace " Kiyi haƙuri Ainu..nasan ba laifin ki bane ,nayi kuskure dana jefe ki da wannan kalam, kiyi mun afuwa! Nasan...kamin ya ƙare maganan ne ta juya masa baya tare da jan bargon ta ,kasantuwar weather ɗin da muke ciki na sanyi ...mu tashi lafiya shine abun da tace tana juyawa tare da rufe idanun ta kaman mai barci ,amma kuma sam ba barcin take yi ba , damuwa da abubuwa da yawa da suka faru suka shiɗe take tunawa a dai dai wannan lokaci.....Waiwaye adon tafiya! Tuna baya!!

Maaama Daddy!!! Muryar Zia ya karaɗe ko ina na cikin wannan gida. Sakin glasscup ɗin dake hannun ta Hajiya Ainu tayi tana fitowa daga Kitchen cikin sauri a tunanin ta wani abu ne ya samu ɗiyar nata ɗaya tilo. Ɓangaren Alhaji Yero da ya gama sanin wacece Zia a hankali ya sauke jaridar hannun sa yana kallon inda Zia take tsaye a kan stairs ɗin falon. Dafe ƙirji Hajiya Ainu tayi cike da Son jin lafiya wannan kira da tsakar rana tace ' Zia!! Kecewa da dariya yarinyar tayi wanda ashekaru baxata haura 7 zuwa taƙwas ba , murmushi tayi tana faɗin i love You Maama! I love Daddy!! I lab u both.... Murmushi Hajiya Ainu tayi kamin suyi magana Zia tayi ɗakin ta da gudu cike da ƙiriniya ta haye stairs ɗin....I lab you much my dear daughter. Cewan Alhaji Yero . Itako Hajiya Ainu juyawa tayi tana girgiza kai cike da jin Son ɗayar nata ainun.

***

Safiyar Lahadi wannan rana ,ranace da duka suke gida kasantuwar weekend , Zaune suke duk familyn Wato Hajiya Ainu da Alh Yero sai kuma ɗiyar tasu Zia ,wacce take kusa da ƙafan mahaifin nata tana akan carpet ɗin dake ƙasa , gaba ɗaya hankalin ta na akan ɗan mini laptop ɗin ta pink na Yara ,Wanda babu abun da take yi sai playing games . Ƙarar buɗewar Gate ne yasata miƙewa da gudu tana tsalle da tafi na yara tare da cewa" Yeeeee Daddy gamai photographer Nan yazo! Suna a haka ne sai ga sallamar mai hoton da suka ɗauko shi musamman a wannan weekend don Jin dadin wannan a hali... A haka kullum suke rayuwa , cike da jin dadi da walwala da kuma ƙwanciyar hankali. A wata Ranan Monday ne Zia sai tuƙuƙi take tana haɗe gira sama da ƙasa ,ƙamin Alh Yero da yake miƙo mata school bag ɗin ta yace " Lele na waya taɓa mun ke?. Kaman ko jira take cike da Muryar yara da hauka tace " Bakai ne ba Daddy ,Kullum baƙwa kawoni wuri zuwa school I'm always coming late Dad! One period nake rasa kullum...meye matsalar Maama da Daddy ne?. Murmushi yayi yana dafata kamin yace " lele na azo lafiya bashi ne ba?. Eh to amma nidai yau ya kamata kayi magana Da Vp . A haka a wannan rana sai da Alhaji Yero yakaita sukayi mata da Vice sannan ya samu sukuni...

Shigar Hajiya Ainu siyasa shi ne musababbin faruwar komai tun daga salsila. Ranan da baxasu taɓa mantawa ba itace wannan rana ,wacce Hajiya Didi Mahaifiyar Alh Yero tayo kirar su da tsakar rana akan tijara da fitina nata. A wannan Rana Hjy Ainu tayi kuka ta gode Allah akan zagi da tijarar da tasha na Hajiya Didi ,tana cewa ta gama mata da ɗa ,kuma Aure zai ƙara zaya Auri yʻarʻ uwan sa da suke yʻayʻa maza . Dama ta daɗe bata haihuwa ba , sai da tafi shekara goma ,gashi tun da ta haifi ɗaya zia wato Zainab mai sunan Hajiya Didi bata ƙara haihuwa ba. Tana bukatar jikoki da yawa yayyame da ita don haka Aure zaiyi. Wannan magana ya ɗaga hankalin Hajiya Ainu da mijin nata wanda yake shahararren ɗan kasuwa kuma ɗan dangi ,don dangin Alh Yero Auren hadi suke ,akan shi ya fara auro bare kuma SADAKA YALLA,wannan yasa Sam Hajiya Ainu bata da fari a idon Hajiya Didi. Da wuraren yammaci suka baro gidan dan Hjy Didi da yake gaskiya layout. Maama Maama!!! Zia ta Kira sunan ta kusan sau uku ,kamin Hjy Ainu ta juya tana saurin ɓoye damuwar ta...Maama meye Sadaka Yallah? Hajiya Grandma duk idan tana son Saki kuka sai tace maki Sadaka Yalla! Meye shi Maama?. Cikin ƙaƙalo murmushi Na dole kawai sai hawaye ya fara wanke ma wa Hjy Ainu idanu , No my baby! Don't put it on ur mind Zia. Ba komai , nice Sadaka yalla Kar ki manta ko gaba ko me kika zama kika gansu suna Bara a titi kar ki ƙyamace su nima Sadaka Yalla ce Maaman ki.....ƙiiiiiiiƙuuuuuuuuuuu kawai kakaji a tsakiyar ƙwalta titin tsakanin ɗan Magaji gaskiya.....Wata babban moto ce ta shigar masu gaba , wanda moton nasu sama tayi kawai sai tayi cikin wani ƙwatantazo....wannan kenan! Gigif Hajiya Ainu ta tashi daga ƙwancen da take sunan Zia kawai take ambato ,Wanda cikin sauri Alh Yero ya kamata yana rungume ta jikin shi tare da fara mata Addu'oi , don yasan Abun da ya tada ita cikin kiɗima tuno da abubuwan da suka faru shekaru goma da suka wuce

ne. Rungume shi tayi tsam tana fashewa da kuka mai ban tausayi da ƙaryar da zuciya ....

❁❁✿✿

RUGAR KIDANDAN kuwa komai sai dai muce Alhmdllh, domin kuwa sun samu sauƙi daga dukkan wasu masu kawo masu hari. Ƙwana biyu aka yi ana mawa Shatu riƙiya a tunanin su jinnu ne suka shafeta duba ga yanayin weather n. Haka ta ƙwana huɗu bata fita ko ina ,kullum tana kewayen bukkan . Shiko Abdul Ahaad tun bayar rabuwar sa da Shatu su Nura da Samir suka fara ce masa mijin yar Fulani da sokana iri iri...wai saboda bada kula har ruga yakai ta...Kai tun baya tunanin yarinyar yafara tunanin ta a zuciyar shi .... A ranan da yakai kwanan su Baƙwai ne da haduwa da kansa ba tare da kowa ya sani ba ya nufi cikin rugar...acan gyefe ya tsaya inda babu mai hango sa....Shatu ya gani a tsakiya anyi da ira ,wani mai waƙar shantu da irin ƙoroson nan na mutan jeji yana bugawa ita kuma sai rawa take tana juya jiki kaman wanda babu ƙashi a jikin ta... Wani dariya Ne Abdul keyi wanda shi kan shi bai Son ya iya wannan dariya ba. Ganin yanda Shatu ke rawar hauka ,ita a dole wai Rawa take shiko mai ƙoroso sai ambaton sunan ta yake yana buga shantu mai kama da ƙwarya. Zokaga fulanin rugar yanda suka yi rumfa suka rufe wurin kowa na bin Shatu da kallon burgewa...a takaice a haka Abdul Ahaad ya shagalta wanda bai koma jejin su ba sai yammaci.....

❁❁✿✿

A washe gari ne tun safe Shatu tayi shirin fita kasuwa don ƙwarya uku ta cika da nono tana ɗaurasu duka akan ta ... Kamun rana ta fito tuni ta isa cikin garin Zaria ,yan nono dake anan tudun Wada . Tun daga isowan ta masu adaidaita da suke zama a wurin suna jirar masu hawa suka fara tsokanan don sun san ta da surutu suna cewa ":a'a yau fulfulbe ne da kan ta,Allah yayi maku fitowa daga hannun kidnpers .Harara ta watsa mawa ɗan liti dake tsokanan ta ,dariya yasa yana cewa " Haba Shatu me yayi zafi? Shawara kar ki koma Ni zan baki gida na kiyi zama da Matana a can. Kin guje mawa....kai ɗan liti ya isa...Ai to Allah yakawo mana wasu sojoji masu kama da Samudawa...ka gansu ne? Ai dole ɓarayin nan su gudu. Zaro ido Ɗan liti yayi yana cewa " Ai Shatu naji labari...Allah dai yasa bakiyi gudu gwari ba...su yan kidnp sun gudu ,ke kuma wani sojan ya ɗauke ki ya gudu dake.... Kallon shashasha tayi masa tana sauke ƙwaryar ta ,tare da fara sayar da nonon . Kamin kace kobo saboda Shatu yarinya ce mai surutu ga sokana sosai take da farin jini kowa na Son ta...tana zuwa da nono kaman ta zubar tuni ya ƙare . Harhaɗa ƙwaryar take a wuri ɗaya kamin ta juya ta kalli Rabi dake kusa da ita...duk idan an ci abu a bata ,ita ba sayar da nonon take ba. Abun ka ga Shatu baki baya iya gani yayi

shiru , cewa tayi " Ohh ke Rabi a haka zaki ƙare ,kullum bakya sana'a sai zaman jirar wani yaci ya baki?. Kema ya kamata ki na rinƙa ɗauko nono kina sayarwa daga rugar ku. Kallon ta Rabi tayi sai a hankali tace "Shatu ai Ni bana da kowa anan!. A'a ke ba Fulani bace?. Shatu tayi maganan tana aje ƙwarya tare da Son Jin Amsa. Gyaɗa kai Rabi tayi alamun eh kamin tace " Ni Fulani ce Amma ta buzaye.ba anan Nigeria nake ba ,ragowar nayi daga ƙasar mu... Ni sadaka Yalla ce! Wani irin bugawa Shatu taji ƙirjin ta yayi....kan ta ne ya wani irin juya mata yana mata gab³ wanda bata taɓa jin irin wannan juyin ba... Dafe kan ta tayi da ƙwaƙwalwa r ta ke juya mata....Ganin ta dafe kai yasa Rabi saurin kama ta tana faɗin Shatu lafiyar ki? . Kusan minti ɗaya tayi bata ce komai ba ,sai can ta nisa tana cewa " Ni ji nayi kaman na taɓa jin wannan sunan Me kika ce? Ɗan maimaita mun...

#Share

Free page zai ƙare a page 10 ku hanzarta wajen mallakar taku ... regular payment₦300 VIP ₦500 SPC ₦1000 via 6037312299 Mohammed Aisha keystone bank ko ki tura katin MTN ta wannan number 08081202932

[11/7, 12:10 PM] ANTY AISHA MMN TEDDY: *SADAKA YALLA!*

(Baraa ko karuwanci! Funny, romantic and sympathy story)ọ

008

Masu buƙatar duk ka littafaina zasu na same su complete Inshaallh

Walijaam₦300

Siyasata₦300

Gidan ƙwarata₦200

Yʼar Aiki na₦100

Dijama yʻar Fulani ₦200

My lady boss₦500

Yʻar maula ₦300

Kʻwarton manya #500

Bintoto

Taɓara₦500

Kawaliya₦300

Zuma da madʻaci₦200

Kʻwaryar sama₦300

Gidan zawarawa₦300

Bafullatanan Ruga₦200

Habibi da'iman da dai sauran su;

❁❁✿✿

Sadaka Yalla Mana Rabi ta kuma nanata mata a karo na biyu....shiru shatu tayi tana faɗawa wani tunanin ta dabam ,wanda ganin hakan yasa Rabi cewa " Shatu tunanin me ne kikeyi haka?. Yamma nayi ya kamata ki koma rugar ku kamin gari ya rufa. Hummmm nisawa Shatu tayi tana miƙewa tare da ɗaukar ƙwaryakun nata da ta tattara su wuri guda. Har ta yi gaba sai kuma ta juyo tana ce mawa Rabi " Yanzu Rabi ke anan zaki ƙwana kenan ,baku da buka irin namu? . Murmushi Rabi tayi cikin mai da damuwar ta ta hanyar nuna komai ba komai ba tace " Eie Shatu anan dama muka saba ƙwana kinga can ƙarƙashin kadan kubanni anan nake kwana kullum , koda kin taho gobe bana nan kika zo can zaki same Ni . Gyaɗa mata kai Shatu tayi alamun to, kana ta juya don nufar rugar Kidandan kai tsaye.

***

Saukar ta kenan daga filin jirgin Aviation dake nan cikin garin Zaria...fuskar ta kacame babu harka ,babu kuma alamun mai wannan fuskar tasan wani abu wai shi kirki ,kallo ɗaya zaka yi mata kasan irin wa'anan yaran ne yʻayʻan manya marasa mutunci tijarar ru ,wanda basa ganin kiman talaka sam. Idon kowa na wannan

Aviation na akan ta ,ganin sunan tana gida nageria ne ,amma shigar ta duk ya sha banban dana mutanen ƙasan. Shiga ne tayi shi irin na turawa , duk da kasancewar tasa doguwar riga ce mai launin milk ta kuma yane kanta cikin ƙaramin mayafin rigar. Malfa ta ɗaura kalon dressing ɗin nata tana fara takowa izuwa inda take hangar drivern da ya taho ɗaukar ta . Barka da isowa Madam Layla! . Drivern yayi maganan tare da ɗan risinawa na girma yana buɗe mata murfin moton , Kallon shi tayi tana kauda kai kaman bata ji mai yace ba, tana shigewa moton cikin yatsini da rashin mutunci. Ɗan tsaki tayi dai dai yana rufo murfin moton tare da shiga mazaunin sa yana fara driving. Kusan mintuna biyar batace masa komai ba ,duk da Tambayar dake cikin ta Issa ya hanata tambayar a tunanin ta tayi hakan ƙaskanci ne. Kai Waya baka izinin tahowa ka ɗauko Ni ?. Tayi maganan tana wani irin hura hanci na tijara ,cikin sauri Drivern yace " Afuwan Hajiya , Hajiya Ammie ne ta aiko Ni.

Ammie! Ta nanata tana kallon sa cike da mmki tace " Ba Yah Abdul Ahaad Ya dawo ba? Shi basai yazo ba kaine za'a turo ka ɗauke Ni dawowata kenan daga abroad ban to tazali da kowa ba sai bagidaje ƙazami irin ka...ji fa yanda ka cika moton duk da tsami rabon ka da wanka kwana nawa??? Tayi maganan tana kashe shi da ido ta mirror ɗin dake hasko masa fuskar ta ta baya. Duk da maganan nata ya sosa ransa ,amma inda sabo ya saba da cin mutuncin ta... Kiyi haƙuri Hajiya Baya garin ne , sakamakon tura su jejin Kidandan da akayi. What?? Inalallahi wai'ina ilaihir rajiun...au har yanzu ba'a bar mun shi sukuni ba? Ina Hajiya Baaba ta ke? Har tabar Abdul ya kuma komawa halaka? Kai da Allah kayi sauri ka kaini gida yanxu ...sam baxan yarda a kashe mun Miji ba a banza a wofi akan wasu talakawa mara galihu dabbobi. Tun da ta fara maganan Shidai drivern bai ce mata komai ba sai jikin sa dake tsuma na tsoro , don fitinan ta abun tsoro ce , tasha ɗauke ma'aikata da mari ba ɗaya ba biyu ba.... Wannan yasa Drivan saurin ɗaga kai Muryar sa har makerketa yake yace " Eh Hajiya. Shiru tayi bai ƙara jin tace komai ba...sai can kaman ance ya kalleta ta madubi yaga Layla sai sharce hawaye take tare da jan majina. Yau na tabbatarwa cewa ' Su Abie basa ƙaunan Yah Abdul ,yabar sojan nan kuma don dole sai su saka ya koma aikin sa... Bayan da ance Ni za'a ɗaura masa ,na bishi can London mu koma da zama! Dole asan mai yiwuwa bazan yarda ba gaskiya sam.....

****

Kamin Shatu takai Ruga Kam Yammaci tayi don Rana har ta faɗa gari ya fara duhuwa. Baaba kam a waje ta tsaya da yar titilan aci balbal ɗin ta ,tana zaman jirar isowar Shatu , don hankalin ta tashi yake ƙwarai idan takai wannan lokacin bata iso ruga ba. Tun daga nesa ta hango hasken acibal bal bal ɗin baaban fulfulbe. Murmushi Shatu keyi tun daga nesa take ƙwaɗa kirar Gwagwgwo na dawo! Kamin

wani lokaci tuni kowa na rugar yasan da dawowan Shatu. Don yanda take wage murya ko yaron goye ne sai yasan da dawowan ta. Zuciyar Baaban fulfulbe ne yayi sanyi cike da jin daɗi take faɗin Yauwa yar Amanan Gwaggo . Ƙarakowa tayi tana riƙe Baaba a tare suka nufa buka... Ƙwaryar nono na musamman da ta tanadar mata ta ɗaga ƙasan gadon kaban da suke kwana tare baaba na ɗauko mata da liddayi. Fura ta ɗauko mata tana ajewa a gaban inda Shatu tayi warwas ta mike ƙafa na gajiya . Cikin salɓi na Fulani Baaba ta fara mata damun tana yi tana tambayar ta ya kasuwa...anan ko Shatu tafara kora mata labari har da na ƙawarta Rabi , miƙa mata furar tayi Shatu na amsa da hannu biyu tana cewa " Yowa Gwaggo ko Rabi zata taho muna zama tare dake anan .

